USAID
FROM THE AMERICAN PEOPLE

Nigeria Reading and Access Research Activity
Primary 2 Pupil Reading Book

Littafin Karatun Dalibai

Aji 2





USAID
FROM THE AMERICAN PEOPLE

Nigeria Reading and Access Research Activity
Primary 2 Pupil Reading Book

Littafin Karatun Dalibai

Aji 2

This early grade reading material is made possible by the support of the American people through the United States Agency for International Development (USAID) under the Nigeria Reading and Access Research Activity (EdData Task Order Number 26, EHC-E-00-04-00004-00) implemented by RTI International.

First edition, 2014

Second edition, 2015

Rights and permissions

The text and illustrations in this work are licensed under the Creative Commons Attribution 4.0 International License. To view a copy of this license, visit http://creativecommons.org/licenses/by/4.0/.

Under the Creative Commons Attribution license, you are free to copy, distribute, transmit, and adapt the work as long as you attribute or credit the original author or illustrator. In the case of this book, please use the following attribution language: "Originally developed under the Nigeria Reading Access and Research Activity and licensed under the Creative Commons Attribution 4.0 International License."

Abubuwan da Ke Ciki

Godiya i

Waɗanda Suka Bayar da Gudummawa ii

Bayanin Taurarin da Ke Cikin Littafin da Tsarinsu iii

Tsarin Jagorancin Ayyuka Na Darussan Makwanni 25 viii

Salsalar Iyali da Dangantakarsu x

Zango Na 1 1

Mako Na 1 2
Mako Na 2 4
Mako Na 3 6
Mako Na 4 8
Mako Na 5 10
Mako Na 6 12
Mako Na 7 14
Mako Na 8 16

Zango Na 2 19

Mako Na 1 20
Mako Na 2 22
Mako Na 3 24
Mako Na 4 26
Mako Na 5 28
Mako Na 6 30
Mako Na 7 32
Mako Na 8 34

Abubuwan da Ke Ciki

Zango Na 3 37

Mako Na 1 38
Mako Na 2 40
Mako Na 3 42
Mako Na 4 44
Mako Na 5 46
Mako Na 6 48
Mako Na 7 50
Mako Na 8 52
Mako Na 9 54

Jadawalin Haruffan Hausa 56

Godiya

Aikin Binciken Karatu da Samun Gurbi (RARA) da Cibiyar Bincike ta RTI ta gudanar, wanda Hukumar Raya Ƙasashe ta Amurka (USAID) ta ɗauki nauyi, na miƙa godiyarta ga dukkan waɗanda suka tallafa wajen samar da **Littafin Karatun Ɗalibai** na Hausa don amfanin aji biyu na firamare. Wannan littafin ya ƙunshi abubuwan da ke cikin manhajar Hausa ta makarantun firamare, wadda ake amfani da ita a makarantun Jihohin Bauchi da Sokoto, kamar yadda Hukumar Bincike da Bunƙasa Ilimi (NERDC 2012), ta samar.

Haka kuma, muna godiya ga Ma'aikata Ilimi da Hukumar Ba Da Ilimin Bai-Ɗaya (SUBEB) na jihohin Bauchi da Sokoto, domin ba da gudummawar ma'aikata da shawarwari, wanda ya tabbatar da aiwatar da ayyukanmu cikin sauƙi.

Daga ƙarshe, muna jinjina wa ilahirin marubuta da editoci da mazayyana hotuna da ma'aikatan bayan fage, waɗanda suka sha famar aiki wajen samar da littafin a cikin harshen Hausa. Godiya ta musamman zuwa ga ƙwararru, kamar Kwamitin Ba da Shawara Kan Koyar da Karatu (RAC/RTWG) na Jihohin Bauchi da Sokoto, waɗanda suka taimaka wajen samar da wannan **Littafin Karatun Ɗalibai.**

Waɗanda Suka Bayar da Gudummawa

Sunaye	Wurin Aiki
Ahmad Alh. Umar	State Universal Basic Education Board (SUBEB), Sokoto
Alison Pflepsen	RTI International
Akanbi John	Illustration Consultant
Bilyaminu Bello Inuwa	Nigeria Reading and Access Research Activity (NRARA)
Ɗahiru Yalwa Mohammed	College of Education, Azare
Dubeck, Margaret	RTI International
Godwin Ondoma	Desktop Publishing Consultant
Hadiza Salihu Koko	Shehu Shagari College of Education, Sokoto
Lauwali Ibrahim	State Universal Basic Education Board (SUBEB) Sokoto; Bodinga LGEA
Muhammadu Bello Yusuf	Nigeria Reading and Access Research Activity (NRARA)
Phyllis Hildebrandt	Technical Advisor (Consultant)
Prof. Malami Buba	Hausa Language Consultant
R. Drake Warrick	Nigeria Reading and Access Research Activity (NRARA)
Raphael Aiyedipe	Nigeria Reading and Access Research Activity (NRARA)
Safiya Bala	State Universal Basic Education Board (SUBEB) Bauchi; Bauchi LGEA
Salisu Abdullahi Tsiga	Hausa Language Consultant
Swadchet Sankey	Nigeria Reading and Access Research Activity (NRARA)
Yahaya A. Umar	State Universal Basic Education Board (SUBEB), Bauchi
Zahra'u Abubakar Maishanu	Nigeria Reading and Access Research Activity (NRARA)

Bayanin Taurarin da Ke Cikin Littafin da Tsarinsu

1.0. Bayanin Littafin Karatun Ɗalibai:

An tanadi wannan littafin domin makarantu 60 da aka zaɓa don yin binciken iya karatu da kuma yanayin gudanarwarsu. An zayyana littafin ne domin ya taimaka wajen koyon karatu da rubutun Hausa a aji 2 na firamare.

2.0. Waɗanda Aka Yi Dominsu:

- Ginshiƙai daga ciki su ne, malamai da ɗaliban makarantun nan 60 da aka zaɓa domin yin bincike a jihohin Bauchi da Sokoto.
- Sauran kuwa su ne, kwamitocin gudanarwa na makaratun nan 60 da ƙungiyoyin malamai da iyayen yara da ofisoshin ilimi na ƙananan hukumomi da makarantun firamare da hukumomin ba da ilimin bai-ɗaya na jihohi da kuma ma'aikatun ilimi na jihohi.

3.0. Halayya da Ɗabi'u Gama Gari Na Waɗanda Aka Yi Dominsu:

- Malamai: Zuwa kasuwa da hulɗa da abokai da 'yan uwa da Sallah a masallaci da zuwa wurin bukukuwa kamar su ɗaurin aure da zanen suna da bikin sallah da sasanta husuma a tsakanin al'umma da zuwa wajen wasannin motsa jiki.
- Ɗalibai:Talla bayan tashi daga makaranta da zuwa makarantun allo da kasuwa da noma da koyon sana'a da wasan ƙwallon ƙafa da wake-wake da raye-raye da 'yar gala-gala da wasan tsalle da langa da yin jirgin leda da wasa da shi da kuma gara gare.

Taurari da Ɗabi'unsu

Nana, 'yar shekara bakwai (7) ce. Girman Nana ya wuce na shekarunta domin kuwa kusan tsayinsu ɗaya da yayanta Abba. Nana siririya ce, baka mai fararen idanu da kuma kitson zanen yawo a kanta. Wani abu da ya bambanta ta da sauran yara shi ne tana da wushirya a hakoranta. A kodayaushe takan sa riga 'yar kanti da zane da koren hijabi. Tufafinta na makaranta kuwa, riga ce da wando masu launin kasa-kasa da kuma farin hijabi.

Nana

Nana yarinya ce mai kwakwa da son koyon sababbin abubuwa, musamman daga wajen kakarta wadda take yawan taimakawa. Tana sha'awar dabbobi wanda a lokacin da ba ta da aiki, takan yi wasa da wasu daga cikin dabbobinsu na gida. Nana na zama a wajen kakanninta, kuma tana taimaka musu wajen aikin gida. Nana ta shaku da iyayenta da kuma yayanta Abba, domin suna yawan ziyartarta.

Abubuwan da Take So:

Nana na son karatu da wasan gala-gala da kuma zuwa kasuwa. Tana da kwakwa da kuma son yin kwalliya. Nana na jin dadi cewa kakarta na koya mata saka. A matsayinta na yarinya mai hankali da hazaka tana so ta ga ta kare aikinta na makaranta domin ta saurari labaru daga Kaka. A makaranta kuwa, tana son lokacin tara, domin ta yi wasa da kawarta Amina, wadda gidajensu ke kusa da juna. Darasin da Nana ta fi so shi ne lissafi.

Abubuwan da Ba Ta So:

Nana ba ta so a tsokane ta kuma ba ta son yin talla.

Abba shi ne yayan Nana, kuma shekarunsa tara (9). Kusan tsayin Abba ɗaya da ƙanwarsa Nana. Abba kamar Nana, baki ne, siriri da fararen idanu. Yana kama da Nana sosai ta wurare da dama, domin shi ma yana da wushirya, amma ba ta kai faɗin ta Nana ba. Yayin da Nana ke da son jama'a, shi Abba ɗan shiru-shiru ne. Akan iya bayyana shi da yaro mai kunya kuma kamili. Wani babban halin da za a iya bambance Abba da shi, shi ne, yana da matuƙar tsafta. Abba yana jin daɗin ziyarar Nana a gidan Kaka, domin yana taimakawa wajen yin aikin gona da kuma wasa da dabbobin gidan su Kaka. Abba ya shaku da Nana domin haka yake yawan ziyartarta tare da iyayensu.

Abubuwan da Yake So:

Abba na son yin jirgin leda da kuma wasa da shi a filin wasa, yana kuma son hawan kekensa. Abba na son yin wasa da kyanwar gidansu, amma kuma ya fi son zuwa gona da kuma yin wasa da dabbobi a duk lokacin da ya ziyarci Nana a gidan kaka.

Abubuwan da Ba Ya So:

Abba ma ba ya son a tsokane shi. Ya fi son ya yi 'yan guje-gujensa a kan ya zauna wuri ɗaya yana sauraren labari.



Abba

Manyan Abokansu

Amina

Babbar ƙawar Nana ita ce Amina. Ba kamar Nana ba, Amina na da ɗan jiki da kuma ‘yan kumatu, sannan kuma fara ce. Amina na da ƙokari da kuma saurin tafiya. Yawancin lokuta za a ga Amina a cikin doguwar riga shuɗiya da hijabi.

Ali

Babban abokin Abba shi ne Ali. Ali ya fi Abba tsayi kuma yana yawan sa kaftani mai kalar madara. Ba kamar Abba ba, Ali yaro ne mai son shiga jama’a yana kuma ƙokari ya ga Abba ya zama kamar shi.

Kauyen Bausa

Kaka da Kaka

- Kasuwar ƙauyen Bausa na ci kowace Asabar.
- Kauyen ya shahara wajen noma da kiwon shanu.
- Harsunan da aka fi amfani da su a ƙauyen su ne Hausa da Fulatanci.
- Akwai ɗakin shan magani da makaranta da kuma dandali da filin wasa.

Garin Ringimi

Mama da Baba

- Ringimi birni ne inda iyayen Abba da Nana suka koma da zama, domin aikin gwamnati.
- Mutanen Bausa da wasu ƙauyuka na zama a Ringimi domin aiki, amma kuma ba su manta da gida ba.
- Maƙwabtan gidan su Abba, su ma daga Bausa suka zo, kuma dukkaninsu Hausa ko Fulatanci suke yi.
- Nisan Ringimi zuwa Bausa, tafiyar awa ɗaya ce kawai.

Tsarin Jagorancin Ayyuka Na Darussan Makwanni 25

	Jigo	Tsari	Taurari	Aiki
1	Gida - Iyali	Gidan Kaka a Bausa	Nana/Amina	Nana na wasan gala-gala
2	Gida - Iyali	Gidan Kaka a Bausa	Nana/Kaka	Kaka na toya masa
3	Gida - Iyali	Gidan Kaka a Bausa	Nana/Kaka/ Mama	Kaka ta ce wa Nana ta je tallar masa
4	Gida - Iyali	Gidan Kaka a Bausa	Nana/Kaka	Nana na saka wa Baba hula
5	Gida - Muhalli	Gidan Kaka a Bausa	Nana/Amina	Nana da Amina na rini
6	Gida - Muhalli	Gidan Kaka a Bausa	Nana/Kaka	Kaka na daka dawa
7	Gida - Muhalli	Gidan Kaka a Bausa	Nana/Kaka	Kaka na ba da labari
8	Gida - Muhalli	Gidan Ringimi	Abba	Abba na share gida
9	Makaranta – Filin Wasa	Filin wasan makaranta a Bausa	Nana/Amina / Abba/Baba	Nana da Amina na waka da wasa
10	Makaranta – Filin Wasa	Dandalin wasa a Bausa	Nana/Amina	Bikin Sallah
11	Makaranta – Filin Wasa	Dandalin wasa a Bausa	Ali/Abba	Zuwa kallon wasan kokawa
12	Makaranta – Filin Wasa	Dandalin wasa a Bausa	Ali/Abba/Nana/ Amina	Yawon Sallah
13	Makaranta - Aji	Filin makaranta a Bausa	Nana/Amina	Cikin filin makaranta da littattafai
14	Makaranta - Aji	Ajin makaranta a Bausa	Amina/Nana	Cinnaka ya ciji Amina
15	Makaranta - Aji	Makarantar Ringimi	Abba/Ali	Abba da Ali na hutawa, sauran yara na wasa a wajen aji
16	Makaranta - Aji	Makarantar Ringimi	Abba/Ali	Abba na cin shinkafa, sauran yara na hayaniya a aji
17	Al’umma - Kasuwa	Kasuwar Bausa	Nana/Amina	Sayayya a kasuwa

	Jigo	Tsari	Taurari	Aiki
18	Al'umma - Kasuwa	ƙauyen Bausa	Kaka/Abba	Girbin dawa don sayarwa a kasuwa
19	Al'umma - Kasuwa	ƙauyen Bausa	Kaka	Tafiya da jaki domin saye da sayarwa
20	Al'umma - Kasuwa	ƙauyen Bausa	Nana	Nana na korar zakara da gudu
21	Al'umma - Sufiri	Kasuwar Ringimi	Baba/Mama	Dawowa daga kasuwa a cikin mota
22	Al'umma - Sufiri	Kasuwar Bausa	Kaka	Kaka za ta je kasuwa domin sayar da kayanta
23	Al'umma - Sufiri	Kasuwar Bausa	Mama	Mama da Nana a kasuwa
24	Al'umma - Sufiri	Kasuwar Bausa	Kaka	Kaka da jaki a hanya kasuwa
25	Gida - Iyali	Gidan Kaka a Bausa	Nana/Kaka/ Amina	Nana ta gano ɓaɓaryar Kaka

Salsalar Iyali da Dangantakarsu

Kaka

Kaka

Mama

Baba

Nana

Abba

Amina

Ali

ZANGO NA 1
Mako 1 - 8
Darasi 1 - 16

Nn Aa

na an nan

Nana na ana

Nana na gida.

N n N n N n

A a A a A a

N a A n n a n



Karatun labari

Nana na nan.

Nana na gida.

Nana na wasan gala-gala.

Kk Aa



ka na

kaka kana naka

Kaka na masa.

K k K k K k

A a A a A a

K a A k k a



Karatun labari

Kaka na gida.

Kaka na masa.

Nana na kallo.

Mm Aa



ma am na

mama amma nama

Mama na cin nama.

M m M m M m

A a A a A a

M a A m m a

Karatun labari

Mama na gida.

Mama na cin nama.

Nana na masa.

Ss Aa



sa ma na

kasa sama nasa

Nana na saka.

S s S s S s

A a A a A a

S a A s s a



Karatun labari

Nana na saka.

Nana ta saka hula.

Hula na saman tebur.

Rr Ii



ra ri

rina rana rini

Nana na rina riga.

R R r r R r

I i I I i I

R i I r i R

Karatun labari

Rana ta fito.

Nana na rina riga.

Amina na rina riga.

Dd Ii

di da mi

damina dami daka

Nana na gyara dami.

D d d D d D

I i I I i I

D i I d i I



Karatun labari

Kaka na daka dawa.

Nana na gyara dami.

Sai ga mage.

Tt Ii

ti ta

mata titi tasa

Tana rike da tasa.





Karatun labari

Kaka na kan tabarma.

Nana na kan turmi.

Tana riƙe da tasa.

Ts ts Ii

tsa tsi ni

tsakani tsinka tsanani

Abba na da tsananin tsafta.

Ts ts Ts ts

I i I I i I

Ts I i ts i

Karatun labari

Abba na da tsintsiya.

Abba na shara.

Abba na da tsananin tsafta.



ZANGO NA 2
Mako 1 - 8
Darasi 1 - 16

Bb Aa

ba bab ni

baba babba babana



Baba da Abba na wasa.

B b B b B b

A a A a A a

B a b B a b



Karatun labari

Abba a babban fili.
Baba da Abba na wasa.
Nana da Amina na wasa.
Kowa na wasa a fili.

Ww Aa

wa sa san

wasa wata wanka

Nana ta yi wanka.

W w W w

A a A a A a

W a A w a



Karatun labari

Jiya an ga watan Sallah.
Nana ta yi wanka.
Nana da Amina na rawa.
Ana wasan sallah.

Gg Ii



gi gan dan

Ringimi gasa ganga

Ana gasar kokawa a Ringimi.

G g G g G

I i I I i I

G i I g i I

Karatun labari

Ana gasar kokawa a Ringimi.

Ana buga ganga.

A gidan su Ali akwai ganga.

Abba na gasar kokawa.

Yy Ii

yi ya wa

yayi iya yawa

Nana ta iya kwalliya.



Karatun labari

Yau ma ana bikin sallah.
Abba na yawon sallah.
Nana ta iya kwalliya.
Amina ma ta iya kwalliya.
Sun sanya kayan yayi.

Ll Uu

lu lun bu

lungu ulu lambu

Amina a lungu cikin lambu.

L l L l L l

U u U u U

L u l U u L

Karatun labari

Amina a lungu cikin lambu.
Tana wasa da ulu.
Ga Nana da littafin karatu.
Sai suka zauna tare.

Cc Ii



ci ki kin

cinnaka cikin abinci

Cinnaka ya ciji Amina.

C c C c C

I i I i I

C i I c I

Karatun labari

Nana da Amina cikin aji.
Amina na cin abinci a aji.
Cinnaka ya ciji Amina.
Amina ta ji ciwo.

Hh Uu



hu la tu

hutu hutawa hula

Ali ya cire hular Abba.

H h H h H

U u U u U

H u U h H u

Karatun labari

Lokacin tara ya yi.
Abba da Ali suna hutawa.
Abba ya sa farar hula.
Ali ya cire hular Abba.
Abba ya ture hannun Ali.

Sh sh Ii

shi sha ru

shayi shiru tashi

Amina ta zo da shayi.

Sh sh Sh sh

I i I i I

Sh i I sh Sh



Karatun labari

Amina ta zo da shayi.
Abba ya zo da shinkafa.
Abba ya zubar da shinkafa.
Yara sun tashi suna surutu.



ZANGO NA 3
Mako 1 - 9
Darasi 1 - 18

Ff Aa

fa ra da



fara dafa fadawa

Sun hadu da fadawa.

F f F f

A a A a A a

F f a A f a

Karatun labari

Ana sayar da fara a kasuwa.
Amina ta sayi fara.
Sun haɗu da fadawa.
Nana ta dafa shinkafa.
Za su kai wa kaka.

Dd Aa

da di gir

dari fadi kafada

Abba ya dauki
dawa a kafadarsa.

D d D d

A a A a A a

D a A d a D

Karatun labari

Lokacin ɗari dawa kan nuna.
Lokacin girbi ya yi.
Kaka da Abba suna gona.
Kaka da Abba suna girbin dawa.
Abba ya ɗauki dawa a kafaɗarsa.

Jj Ee

je ji ja

daji je kujera

Zai je kasuwa da dawa.

J j J j

E e E e E

J e E j e

Karatun labari

Ga Kaka da jakinsa.
Ya jera dawa a bayan jaki.
Zai je kasuwa da dawa.
Jaki ya bi ta daji a guje.
Kaka yana bin jaki a baya.

Zz Oo

zo za ne

zomo zane zakara

A gidan Kaka akwai dabbobi.

Z z Z z

O o O o O

Z o O z o

Karatun labari

A gidan Kaka akwai dabbobi.
Nana na da zomo da zakara.
Zomo na tono a gindin bishiya.
Zakara na cin dawa.
Nana ta kori zakara da gudu.

Kk Uu



ku gu ra

kura tuka kusa

Motar Baba ta
yi kura sosai.

K k K k K

U u U u U

K u k U K u

Karatun labari

Baba da mama a mota.
Suna dawowa daga kasuwa.
Baba yana tuƙa mota.
Motar Baba ta yi ƙura sosai.
Kusa ta fasa tayar motar Baba.

Kw kw Ai ai

kwai kwa ai

kwai kwarya kwarai

Kaka ta dauki
kwai a kwarya.

Kw kw Kw kw

Ai ai Ai ai Ai

Kw kw Ai ai

Karatun labari

Nana na tara ƙwai a ƙwarya.
Kaka da maƙwabtanta za su kasuwa.
Kaka ta ɗauki ƙwai a ƙwarya.
Maƙwabciyarta ta ɗauko ƙwaƙwaƙwa.
Kwaryar Kaka tana da kyau ƙwarai.

Kw kw Ai ai

kwai kwa yo

kwakwa kwaikwayo akwai

Nana na kwaikwayon kwalliyar Mama.

Kw kw Kw kw

Ai ai Ai ai

Ai Kw kw ai

Karatun labari

Nana ta je garin Ringimi.

Mama na kwalliya a cikin ɗaki.

Nana na kwaikwayon kwalliyar Mama.

Sun yi kwalliya za su je kasuwa.

Za su sayo kaji guda bakwai.

Sun ga kwano cike da kwakwa.

Gw gw Au au



gwau gwai za

gwauro gwaza gwaiba

Ya hadu da gwauro a hanya.

Gw gw Gw gw

Au au Au au

Gw au gw Au



Karatun labari

Kaka da jakinsa zai je kasuwa.
Yana ɗauke da buhun gwaza.
Ya haɗu da gwauro a hanya.
Kaka ya dawo daga kasuwa.
Ya sayo wa Nana kwandon gwaiba.

Ɓɓ Aa

ɓa ɓul ɓe

ɓata ɓullowa tabarya

Tabaryar Kaka ta ɓata.

Ɓ ɓ Ɓ ɓ Ɓ

A a A a A

Ɓ a ɓ A Ɓ a

Karatun labari

Tabaryar Kaka ta bata.

Nana da Amina sun fita neman tabarya.

Nana ta gano tabarya a hanyar kasuwa.

Amma tabaryar ta baci a gefe daya.

Kaka ta yi murnar ganin tabaryarta.

Jadawalin Haruffan Hausa

A a	**B b**	**Ɓ ɓ**	**C c**
D d	**Ɗ ɗ**	**E e**	**F f**
G g	**H h**	**I i**	**J j**
K k	**Ƙ ƙ**	**L l**	**M m**
N n	**O o**	**R r**	**S s**
T t	**U u**	**W w**	**Y y**
Z z			

Gw gw	**Gy gy**	**Kw kw**	
ƙw ƙw	**ƙy ƙy**	**Fy fy**	
Ts ts	**Sh sh**	**Ai ai**	**Au au**